Abubuwan da kasa ta kunsa na zahiri – Gwaji na P02

# LA'AKARI DA YANDA TSARIN KASA YAKE[1]

*Taskar la'akari na.4- 7a-8a*

| | |
|---|---|
| MUHIMMANCI | An bayyana tsarin kasa ta yanda guggubin abubuwa da bangalolin sinadarai suka jeru wuri daya. Idan aka dunkule bangalolin sai aga sunyi girma su bada wa nau'i bayyananne. Tsarin kasa yana bayyana wasu muhimman abubuwa kamar yanda tsarin kasa ya zauna, wanda yake nuni da karfin kasa ta yanda yake zata cigaba da zama a yanda take koda kuwa za'a buga mata wani abu ne, koda kuwa na yanda ya kebijirowa ne ko kuma musamman akasa wannan abin ya faru |
| KAYAN AIKI |  Cebur  Fallen roba |
| TSARI | 1) A debo kasa mai fadin 20cm da cebur |
| | 2) Asa fallen roban akan kasa mai tsauri (misali fallen ice). Ajeho kasar daga bisan 1m sau uku akan fallen roban har sai dunkulen kasan ya tarwatse zuwa kananun bangaloli |
| | 3) Asa karfi a hankali a rarrabe wargazazzan kasan nan ta hanyar tura mayan zuwa bangare daya sannan kuma masu laushin bangare daya. A shirya kasan ta hanyar bazata yanda zata mike a kwance ba tare da kwari da tuduba. |
| AMFANIN WANNAN HANYAR | Saukin iya tantancewa ta zahiri tare dayin amfani da kayan aiki yankadan. Ana iya tantance kasar da aka basu kula daban-daban. |
| GAZAWAR WANNAN HANYAR | Akwai adadin kasan da ake son amfani dashi domin tantancewa. Ana iya amfani da wannan hanyan a yanayin jikewan kasa masu yawa, amma yafi kyau a lokacin da kasa danshi ko danshi sosai, kada ayi amfani da kasar da bushe ko ta cika jikewa. |

| TAMBAYOYIN DA ZA'A AMSA | Wadanne siffofi (Yawa, tsari, tauri) na dunkulen kasa ko hoguna? Yaya hanyoyin iskan kasar suke? Menene ya janyo irin wannan tsarin kasa? Kana jin irin yanda ake sarrafa kasar ya janyo irin wannan tsarin kasar? Kayi la'akari da banbance-banbance a kasa daban-daban da/ko kuma yanda ake sarrafa kasar? |
|---|---|

| MISALAN GWAJI | | |
|---|---|---|
| MARA KYAU | MATSAKAICI | MAI KYAU |
| Kasa takan kasance a duddunkule da kuma hoda-hoda. Bashi da ramuka kosai yan kadan wanda yake rage yawan zagayawar iska da sauran al'amuran na kasa, wanda yaje cutar da wanzuwar shukoki | Akwai turbaya masu kusurwa da kuma mabanbantan girma. Shigan jijiyoyi kasa da girman su bazai iya samuwa yanda ya kamata ba saboda babu tsarin kasan da ya kamata | Kasar tana dauke da turbaya da kuma bangaloli masu saukin wargajewa sanna kuma a mulmule suke. Kasar da take da tsari mai kyau tana rage curewan kasa a lokacin da abubuwa kebi ta kanta. Yanayin zagayen iska da kwararan ruwa da kuma rike ruwan a irin wanna kasa sunfi wanzuwa sosai. |
|  © FAO 2008 |  © FAO 2008 |  © FAO 2008 |

1 https://www.fao.org/3/i0007e/i0007e00.pdf